# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Farkon fara samun damuwan Mutum



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Tammy S.**

**Fassarawa: Maren Dameng Daniel**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2020 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

Allah ya halicci komai da komai, lokocin da Allah ya halicci mutum na farko, Adamu, ya zauna a cikin gonar Eden da matar shi, Hauwa'u.  Suna cikin farin ciki  da annashuwa da kuma biyayya ga Allah, sai wata rana na ...





**“Shin ko Allah ya ce,” “kada ku ci daga wani itacen da yake a gonar nan?”  Macijin ya tambaya.  Zamu iya cin komai sai dai ɗan itace kuda ɗaya “ta bashi amsa” idan muka taba ko muka ci zamu mutu “baza ku mutu ba” macijin ya fada .**

Bayan da Hauwa'u tayi rashin ɗa'a ta karya dokan Allah tayi zunubi sai ta rinjayi Adamu ma yaci 'ya'yan itacen.







**A lokocin da Adamu da Hauwa'u sunka yi zunubi, dukkansu sun san da cewa suna tsirara. Sai su ka nemi ganye suka ɗinka bante, su ka kuma ɓuya a cikin daji daga wurin Allah.**

A cikin sanyin yammaci Allah ya zo cikin lambu. Ya kuma san abin da Adamu da Hauwa'u suka yi. Adamu ya daura laifin wa Hauwa'u. Hauwa'u kuma ta daura laifin wa maciji. Sai Allah ya tsine ma macijin, matar kuma za ta ji zafi wurin haihuwa. Adamu domin kayi zunubi, an la'anci kasa da ƙaya da sarƙaƙƙiya sai kasha wahala kafin ka sami abinci.





Sai ubangiji Allah ya kore Adamu da Hauwa'u daga cikin Lambu. Domin sunyi zunubi, an raba su da Allah mai bu sa rai.



Allah ya kuwa sa adda mai wuta ya kore su. Ya kuma mawa Adamu da Hauwa'u rigan sawan fata. Ina ne ubangiji Allah ya samo wanan fatan?

A cikin lokaci, Iyalai sun  fito daga cikin Adamu da Hauwa'u.  Ɗan su na farko, kahilu shi manomi ne.  Ɗan su nabiyui habila shi ma kiyayi ne.  Wata tana ƙabilu ya kawo kyautar abunda ya girba wa Allah.  Habila kuma ya zabo mai kyau da ga cikin dabobin sa, ya ma Allah kyautar hadaya.  Allah kuwa ya ji daɗin kyautar Habila.



**Allah kuwa bai ji daɗin kyautar ƙabila ba sai ƙabila kuwu ya ji haushi. Sai Allah ya ce, “Idan ka yi abu mai kyau, Bazan karɓa bane?”**



Fushin ƙabila bai ƙareba.  Wata rana a fili ya kashe Habila.



**Allah ya kuwa yi magana da ƙabila. “Ina ɗan'uwanka Habila?” “Ban sani ba,” ƙabila ya yi ƙarya. “Ni ke ajiyar ɗan'uwa na?” Sai Allah ya horashi ta wurin karbar basiran sa na noma, ya sa shi ya zama mai yawo barkate.**



Ƙabila ya fita da ga gaɓar ubangiji. Ya yi aure ya auri 'yar gidan Adamu da Hauwa'u. Su ma sun samu lyali. Ba'a jima ba, jikokin ƙabilu da kum tattaba kunne sun cika garin da ya kafa.



**Iyalen Adamu da Hauwa'u sun cika kuwa. A wancan lokacin mutane su na tsawon rai ba kamar yanzu ba.**



Lokacin da ta haifi ɗanta Seti, Hauwa'u tace, “Allah ya bani Seti domin ya maye gurbin Habila.” Seti kuwa mutumin Allah ne, ya yi rayuwa har na tsawon shekaru 912 kuma ya haifi yara da yawa.




A cikin duniya, mutane sun zama masu mugunta daga wannan zuriyyan zuwa wani zuriyan.
A ƙarshe Allah ya ce ya hallaka dukan mutune. Dukkan dabobi da tsuntsaye.
Allah yayi dana sanin halittan mutum. Amma mutum daya
ya gamshi Allah ...


Wanan mutumin sunan sa Nuhu.  Ɗan gidan
Seti, Nuhu kuwa mutumin kirki ne.  Ya yi tafiya
da Allah.  Ya kuma koyawa yaran sa, maza
uku yanda za su biyyya ga Allah.
Yanzu Allah ya shirya
amfani da Nuhu
ta waje na
musamman.

# Farkon fara samun damuwan Mutum

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Farawa 3-6

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da
Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16